


# Samun Ɗaukakar Sa

*Yesu ya ɗauki kunyarmu domin mu sami ɗaukakar Sa*



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Menene akasin kunya? Ina ganin abin da ya fi kusa da kishiyar kunya shi ne ɗaukaka.

> "Gama ya kamance shi, shi wanda abu duka dominsa ne, ta wurinsa kuma abu duka ya ke, garin kawo 'ya'ya da yawa zuwa daraja, shi kamitta shugaban cetonsu ta wurin raɗaɗai,." (Ibraniyawa 2:10)

Lura, Yesu yana kawo 'ya'ya masu yawa zuwa ga ɗaukaka. Ya ɗauki kunyarmu domin mu sami ɗaukakarsa. Wasunmu na da tarihin zama cikin kunya—cike da abubuwan da ba mu iya magancewa, abubuwan da ke bin mu suna kuma damun mu. Waɗannan munanan tunane tunane marasa kyau da tunane tunane masu zafi suna danne mu a lokutan da muke son bauta wa Allah da kuma yabon sa. Ka tuna cewa Yesu, ya kasance tsirara na tsawon sa'oi uku a kan giciye, ya ɗauki kunyar mu gaba ɗaya domin mu sami ɗaukakar Sa.

Na taɓa yin magana a Holland a kan yadda Yesu ya ɗauki , sai wata mace 'yar ƙasar Dutch ta aiko mani da shaidarta a matsayin amsarta. Cewa tun tana ƙarama, an ci zarafinta ta hanyar jima'i—ƙungiyar samari masu fyaɗe—ta kuma ci gaba da fuskantar ƙaskanci ta hanyar jima'i. Daga baya, ta yi aure, amma aurenta bai zama da daɗi ba saboda ɓacin rai da ke cikin zuciyarta game da maza. Ta kasa rabuwa da kunyar abin da ta daure da shi. Daga nan sai Ubangiji ya yi wani abin ban mamaki.

Tana zaune ita kaɗai a ɗakin kwananta, sai ta ga wahayin Yesu a kan giciye, tsirara. Ta fahimci abubuwa biyu: na farko, cewa ya ɗauki kunyarta; na biyu kuma, cewa shi namiji ne. Ko da yake tana da ɓacin rai ga maza, sai ta fahimci cewa namiji ne ya ɗauki hukuncin kunyarta. Wannan ai kyakkyawan abu ne. Ka yi tunani a cikin zuciyarka cewa Yesu, tsirara a kan giciye, ya sha ba'a da zagi daga masu wucewa. Wannan ne babban dalilin gicciye, kuma Yesu ya jure dukan wannan.

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa Yesu ya biya hukuncin kunyarmu, domin ya ɗauki kunyata domin in sami ɗaukakarsa. Amin.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

**Abincin Yini ★**

Kwafi: WD-B097-136-HAU

Sabuntawa ta karshe: 09 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources

